Dukkan abin da yake sa maye haramun ne.

Dada Abu Burdah, daga babansa Abu Musa al’Ash'ari - Allah Ya yarda da shi -: Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya aike shi Yaman, sai ya tambaye shi game da wasu wasu abubun sha waɗanda ake yi su a can, sai ya ce: Waɗanne ne su?, ya ce: «Bit'u da Mirzu». Sai akacewa Abu Burda: Menene Bit'u? Ya ce: Tsimin zuma, Mirzu kuma: Tsimin sha'ir (karamar shinkafa), sai ya ce: «Duk abin da yake sa maye haramun ne» Bukhari ne ya fitar da shi. Kuma Muslim ya fitar da shi da lafazin: Ya ce: Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya aikeni ni da Mu'az zuwa Yaman, sai na ce: Ya Manzon Allah! Lallai akwai wani abin shan da ake yi sa a ƙasarmu ana ce masa: Mirzu daga sha'ir ne, (karanar Shinkafa) da kuma wani abin shan da ake ce masa: Bit'u daga zuma ne, sai ya ce: «Duk abin da yake sa maye haramun ne». A cikin wata riwaya ta Muslim: «Sai ya ce: Duka abin da yasa maye ga sallah to shi haramun ne». A cikin wata riwayar tasa kuma: «Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya kasance haƙiƙa an ba shi matattaran kalmomi da cikarsu, sai ya ce: Ya hana duk abin da yake sa maye wanda ya bugar lokacin sallah».

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi]

Abu Musa al’Ash'ari - Allah Ya yarda da shi - yana bada labarin cewa Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya aike shi Yaman, sai ya tambaye shi game da wasu kayan shaye-shaye waɗanda ake yin su a can, shin su haramun ne, sai ya tambayi Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - game da su. Sai Abu Musa - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Shi ne Bit'u: Tsimin zuma, da Mirzu: Tsimin shinkafa. Sai Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya ce alhali ya kasance haƙiƙa an ba shi matattaran kalmomi: «Duk abin da yake sa maye haramun ne».

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/66536